


An yi wani ɓera baƙauye.

Iyakar yawonsa a

garin ɓera ne.

Wata rana ɓera ya je


birni.




Ɓera ya ga dabbobi daban-daban.

Kule ta ga ɓera.


Ɓera bai taɓa ganin kule ba.



Jikin kule ya ba ɓera shawa.

Ɓera ya je kusa da kule.


Yana son ya shafa jikin kule.



Kule ta yi murmushi.

Bera ma ya yi murmushi.


Bera yana zaton ya sami aboki.



Zakara ya ga wautar ɓera.

Zakara ya matso wurin kule.


Ɓera bai ji daɗin zuwan zakara ba.

Bera ya matsa kusa da kule.


Kule na lashe baki.

Sai zakara ya yi cara mai ƙarfi.



Ɓera ya ruga a guje.

Bai taɓa jin carar zakara ba.





Ɓera ya tsira.

Amma ɓera yana zaton

zakara ne mugu.